Da ba dan kar na tsanantawa muminai ba - ko ga: al'ummata ba - dana umarce su da yin asuwaki a yayin kowace sallah

Daga Abu Huraira - Allah Ya yarda da shi - daga Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: "Da ba dan kar na tsanantawa muminai ba - ko ga: al'ummata ba - dana umarce su da yin asuwaki a yayin kowace sallah".

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya bada labarin cewa shi da ba dan tsoron wahala ga muminai daga al'ummarsa ba da ya wajabta musu yin anfani da asuwaki tare da kowace sallah.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/3364